Education Digital Equity Initiative

# TAKARDAR KOYON KARATU

DABARU MASU SAUKI NA KOYON KARATU DA NA'URORIN ZAMANI (GA DALIBAN DA SUKE MAKARANTUN KARKARA)




Dawainiya:

UK aid from the British people

Foreign, Commonwealth & Development Office

Samarwa:

AREAi

# BAYANI A GAME DA AREAi

An kafa ta a shekarar 2014, aka yi mata rajista a Najeriya da hukumar kula da kamfanoni na CAC na kasa a 2017. Aid for Rural Education Access Initiative (AREAi), kungiya ce mai zaman kan-ta, da ke da manufa, wanda ta ke aiki da makarantu marasa isassun kayan aiki da al'umman da ba su da gata, wajen samarwa 'ya 'yan talaka, marasa galihu da masu karamin karfi kayan aiki da za su taimaka wajen karatu. Tun da aka kafa AREAi, tayi zarra a matsayin daya daga cikin kungiyoyin da suke inganta harkar ilmi, da ya ci burin hada-kai da masu ruwa da tsaki da kungiyoyin gwamnati domin samar da nagartaccen ilmin boko ga 'yan makarantun firamare da sakandare da yaran da suke zaune a kauyukan da suke nesa. Hankalin AREAi ya karkata ne wajen rabawa kowa kayan aiki na zamani, koyon karatu, karatun 'ya 'ya mata, da bunkasa dabarun karatun matasa. Tsare-tsaren kungiyar ya yi tasiri a kan mutane sama da 16, 000 a cikin kauyuka 23 a kusan jihohi 8 a fadin kasar nan.

Shugaban kungiya/babban Darekta: Gideon Olanrewaju
Mataimakin shugaban kungiya: Yetunde Abiodun Omotosho
Ragowar 'yan kungiya: Olajide Charles Falajiki, Godwin Osama, Ifeoluwa Ariyo-Agbaje, da Motunrayo Fatoke
Nauyin daukar hoto: Faje Kashope, Faith Oguche, da Jennifer Bekes
Nauyin zane: Olamide Agunbiade da Aderemi Temitope
Akwatin lambar waya da imel: info@areai4africa.org , +2347061169861
Shafin yanar gizo: www.areai4africa.org; https://equity.areai4africa.org/
Adireshi: Impact Cove, No 4 Sefado Close, unguwar Wuse 2, birnin Abuja, Najeriya.

© 2021



# TSARIN AIKI

Wannan shiri na Education Digital Equity Initiative, aiki ne da aka dauko domin a shawo kan matsalar bambancin da ake nunawa wasu, ta hanyar yada jeringiyar bayanai masu dauke da hujjoji, da kayan karatu masu saukin fahimta da suka zo da bayanai daki-daki ga makarantun kauyuka da karkaran da suka yi nisa da kuma masu karamin karfi a kan yadda za sa su saba da samun kayan karatu na wajen-aji, da ta kafar yanar gizo da kuma samun na'urorin zamani na koyon karatu a wannan lokaci bayan an yi fama da annobar COVID-19. Wannan aiki ya dauki tsarin hada-kai da masu ruwa da tsaki dabam-dabam domin a rika tafiya da kowa ta hanyar bincike da dabarun samun bayanai, tare da wayar da kai a kan fasahan da ake da su da cigaban da ake samu wanda za su iya inganta karatu da samun bayanai wajen talaka da sauran wadanda aka maida saniyar ware. Hukumar birtaniya ta United Kingdom's Foreign, Commonwealth and Development Office ta ke daukar nauyin wannan aiki a karkashin Shirin Prosperity Fund's Digital Access Programme.

# BAYANI GAME DA WANNAN TAKARDAR KOYAR DA KARATU

Wannan takarda ta kawo misalai da yawa na hanyoyin koyarwa na cikin gida domin a taimakawa masu koyon karatu a makarantun kauyuka da karkara da kayan daukar karatu. An kawo bayanin tara (9) daga cikin kafofin koyon karatu daga nesa masu saukin amfani domin a ji dadin rungumar su a ko ina. Ana sa ran cewa amfani da wadannan takarda zai taimaka wajen toshe kafar da ake da ita na damar samun bayanan koyon karatu a cikin al'umma. Ana so jagororin al'umma, iyaye, malamai da shugabannin makaranta su dauki salon da aka kawo a cikin wannan takarda domin tabbatar da cewa yaransu da dalibansu sun samu damar koyon karatu.

## KAFOFIN KOYON KARATU DAGA NESA (NA WAJEN AJI) MASU SAUKIN AIKI

| NA'URA/KAYAN AIKI | WADANDA AKE HARI | AMFANI DA CIKAS | KUDIN DA ZA A KASHE |
|---|---|---|---|
| Rediyo | Daliban firamare da sakandare. | • Babu bukatar yanar gizo.<br>• Na'ura ba za ta iya kai ga kowa.<br>• Za a iya maida martani.<br>• Karbar sakonni ya na iya yin muni | Babu tsada. |
| Talabijin | Daliban firamare da sakandare. | • Babu bukatar yanar gizo.<br>• Ya hada sauti da bidiyo. | Farashinsa ya yi wa dalibi yawa, dole a same shi a kowane gida. |
| Alkalami da litattafai masu magana | Daliban firamare. | • Babu bukatar yanar gizo.<br>• Sun fi komfutar hannu araha.<br>• Ya na bada dama a koyi karatu a harsuna dabam-dabam. | Sayen kunshin ya kai kimanin N30, 000. |
| Gajerun sakonni na SMS | Daliban sakandare. | • Babu bukatar yanar gizo.<br>• Babu bukatar babbar waya. | Za a kashe tsakanin N300 da N500 a duk wata. |
| Kayan koyon karatu a gida | Daliban firamare da sakandare. | • Babu bukatar yanar gizo.<br>• Babu bukatar wata na'ura. | Akwai araha. |
| Manyan wayoyin neman ilmi | Daliban firamare da sakandare. | • Akwai bukatar yanar gizo.<br>• Wayoyi na iya ajiye kaya masu nauyi. | Za a kashe tsakanin N20,000 da N30, 000. |
| Na'urar karanta littafi | Daliban firamare da sakandare. | • Akwai bukatar yanar gizo.<br>• Na'ura na kunshe littatafai, bidiyo da kayan wasa. | Za a kashe kusan N5, 000. |
| V.R | Daliban sakandare. | • Akwai bukatar yanar gizo.<br>• Ba kowa zai iya samu ba. | Farashi zai iya yi wa dalibi tsada, makarantu za su iya samar da shi. |
| Kayan karatun kyauta na yanar gizo | Daliban sakandare. | • Za a iya bukatar yanar gizo. | Amfani da su kyauta ne. |

# Litattafai da alkaluma masu magana

Na'urar littafi da alkalami mai magana ya na dauke da wani irin alkalami na zamani da littafi da aka buga na musamman. Da zarar alkalamin ya taba rubutu ko zanen cikin wannan littafi, sai ya fara karanta abin da aka rubuta, daga ciki har da wasanni, kacici-kaci, da fassara, da sauransu. Littafi da alkalami mai magana ya na taimakawa yara wajen iya karatu da lissafi ta tsarin koyarwar da aka bi. An rubuta littatafin a harsuna irinsu Faransaci, Larabci, Hausa, Ibo da Yarbanci. Yanzu haka akwai shi a Najeriya, kuma za a iya mallakar shi a kan N25, 000.

Idan ana sha'awar sayen littatafai da alkaluma masu magana, za ka iya ziyartar http://maviseducation.com/store/


Malamarmu, tunda aka rufe ma-karanta, yaranmu su ka daina koyon darasin Ingilishi da lissafi. Ko ta ya za ki taimaka mana?
Ka da ku damu Hajiya da Maman Chinoso. Na ma ji labari yaran ba za su iya shiga ajinsu na dandalin sada da zumunta na Zoom da Teams ba.


Wannan na'urar da ke hannuna, ita ake kira alkalami mai magana. Ba ya bukatar amfani da yanar gizo-gizo, don haka Danladi da Chinoso za su iya amfani da shi wajen darasin lissafin da ingilishin su cikin sauki da annashuwa.
Lallai wannan abu yayi! Na ga har wurin saka lasifikar kunne gare shi. Lallai zan so in nemawa Danladi wannan don ya cigaba da karatunsa.


Danladi wai da wannan ne ka cigaba da karatun naka bayan an rufe makaranta?
Shi ne fa, Adewale. Naurar ta kumshi littafai kusan goma wanda na ke amfani da su, kuma har na iya kera jimloli, amsa tambayoyi, da kuma karanta labara. Ina san alkalamin domin ya na Magana da Hausa, Ingilishi, Yarbanci kai har ma da Inyamuranci.
Lallai ya kamata kowane ɗalibi a ajinmu ya san da wannan. Ni ma zan fadawa mahaifiyata ta nemo irin sa.


Barkan ku da dawowa daga hutu mai dogon zango. Ko za ku iya fada mani ta ya ku ka rika karatu a gida a lokacin hutun?


Malama, ni da alkalami mai magana na cigaba da koyon Hausa da Faransanci. Na'urar Mavis Talking Book™ ta kunshi alkalami mai kwakwalwa da littafinsa na musam-man. Idan alkalamin ya ta taɓa rubutu ko hoto a littafin, to zai karanta maka abinda yake wajen. Game da haka kuma, yana da wasanni masu jan hankali, kacici-kacici, fassara, labarai, wakoki da dai sauran su.
Ai kuwa na san wannan alkalamin mai magana. An kirkiro shi tare da hadin gwiwan Hukumar Kula da Jadawalin Najerya. Kowannen ku ya kamata ya mallake shi domin zai taimaka mana wajen darasin mu.

# Fasahar sakonnin SMS da USSD

Yadda ake amfani da shi?

Shin ka san cewa da karamar wayar salular nan mai fitila, wanda ba ta iya hawa shafin yanar gizo, za ka iya tattaunawa da malamai a duk fadin Najeriy? Amma, ta ya ya?

- A Najeriya, za ka iya latsa *347*774# ko *3549# domin samun kayan karatu birjik.
- Za ka iya karanta takardun darasi, ka ziyarci shafin yanar gizo ba tare da intanet ba, ka amsa tambayoyi masu samfurin kacici-kacici da doguwar amsa – duk ta gajeren sako, kuma har ka san kayi daidai ko ba kayi ba.
- Za ka iya biyan har N100 a mako ko N300 a wata domin ka yi amfani da wannan tsarin.
- Za ka iya koyon karatu a cikin harsunan mu na gida, ko ka zabi duk darasi ko maudu'in da ka ke so yayin da ka ke amfani da tsarin USSD ko SMS.


Dalibai, lokacin jarabawan ku ya matso, kuma ba zu mu bude makaranta domin bita ko karatau ba. Sai dai ku yi ta kafar yanar gizo
Toh! Ta ya za mu yi karatu da bita har mu ci jarabawarmu babu na'ura mai kwakwalwa ko wayar zamani?


Ka da ku damu, na san hanyar da za ku bi, ku ci jarabawarku a cikin sauki. Za ku iya amfani da shi har a karamar waya da ba ta da kafar intanet. Daga kun danna *347*774# ko *3549# za ku iya tambayar malamai daga ko ina a Najeriya. za ku iya amfani da littatafan ku tare da bincike a yanar gizo ba tare da ka shiga intanent din ba.


Baba da Allah ina so in yi amfani da wayarka samfurin Nokia 3310 domin yin karatun UTME ta manhajar DigiLearns SMS.


Frank, ina da tambayoyi da yawa daga kara-tun da nake yi a cikin littatafanmu da manha-jar da Mai martaba ya ba mu labari. Za ka iya taimaka mani?


Wannan ai abu ne mai sauki Abdullahi, kawai lambobin za ka latsa a wayarka domin amfani da tsarin 'Tambayi malami' ka tambayi duka malamanmu ashirin. A cikin kasa da mintuna 30 za su ba ka amsa.
Amma tsarin ya burge ni. Ka ce zan iya amfani da tsarin shafin Google in nemo ma'anan kalmomi ba tare da shiga yanar gizo ba


Na tabbata Malam Suleiman zai iya amsa mun wannan tambayar ta Chemistry. Bari in yi amfani da DigiLearns.
A wani mataki ne ruwan Ethanol ya ke tafasa?
Wannan tambaya ce mai kyau daga wurin Frank. Bari in yi sauri in bashi amsa.
Matakin tafasar Eth-anol shi ne a lambar digiri 78.5

# Kayan koyon karatu a gida

Domin tabbatar da cigaban karatun yara a gida, za a iya taimakawa dalibai da kayan daukar darasi, littatafai, da sauran kayan karatu da za su inganta koyon karatunsu ba tare da amfani da shafin yanar gizo ba. Dalibai da kansu ko da taimakon iyayen, malamai, 'yanuwa ko sauran mutane za su iya samar da wadannan kayan aiki. Idan aka tsara kayan karatun da kyau, ya na kunshe da abubuwan da yara za su koya a gida da makaranta.


Yauwa ɗalibai, na amshi sakon ku na cewa kuna so mu taimake mu ku da kayan karatu domin ku cigaba da karatu lokacin kullen Coronovirus, kuma ga kayan karatun.


Yanzu Chidinma dukkkan darasin da ya kamata mu yi a aji ne aka buga mana a takarda domin mu yi karatu a gida?
Nagode Olamide, yanzu zan kai su in tanta-nce su sanan in rabawa dukkannin 'yan ajin.


Yanzu tun da mun samu duka kayan karatunmu an buga mana su, za mu haɗu a wurin karatun unguwar-mu domin mu tattauna tare kafin a dawo makaranta.


Mama, ga kayan karatu na nan, kuma zan karanta yadda shuke-shuke ke hayayyafa, darasin mu da za a koya mana nan gaba a ajin ilmin halittu.
Ka ga banbancin tsirrai masu yaɗuwa su kaɗai da kuma masu yin gicciye nan. Ka gane ko in maka bayani? Ilmin sanin halittu shi ne darasin da na fi so.

# Komfutocin hannu na karatu

Komfutocin hannu watau tablets, wasu na'urorin zamani ne da suke dankare da manhajar daukar ilmi ta musamman da suke dauke da abubuwan da aka tanada domin taimakawa yara wajen samun karatu mai inganci, musamman ga wadanda suke zaune a kauyukan kayau, inda ba a iya hawa shafin yanar gizo da kyau. Akwai na'urorin 'tablets' iri-iri, wasu su na aiki da intanet, wasu kuma su na aiki ko ba tare da intanet ba.

A Najeriya, ULesson ta na cikin misalan komfutocin hannu na neman ilmi da ke taimakawa 'yan makarantun firamare da sakandare. N3, 500 ake kashewa duk wata domin amfani da wannan na'ura, ga daliban da suke mazaunan Najeriya.


Yauwa ɗalibai, ni waklin wata kungiya mai zaman kanta ne. Mun zo mu koya maku yadda za ku yi amfani da komfutar hannu. Akwai darussa kala-kala na ji da kallo duka a ciki. Zai taimaka maku kwarai ku da abokanku wajen yin karatu.


Lallai waɗannnan komfutocin hannun su na da abubuwa masu kayatarwa da za a iya koyan sabab-bin harsuna. Ni yanzu ma koyon faransanci nake yi.
Lallai kam bayanan nasu akwai gamsarwa. Yanzu haka ina kallon yadda mutum zai kare kan sa lokacin annoba.


Wata gudummuwa za ka bamu a matsayinka na shugaban kungiyar iyaye da malamai?
Da ni da wasu iyaye mun yanke shawara mu hada gwuiwa da wata cibiyar koyar na’ura mai kwakwalwa, kuma za mu bada gudummuwan komfutan hannu wanda yaran mu za su yi amfani da shi a gida da makaranta.


Na yi matukar farin ciki ganin cewa zan iya cigaba da karatu duk da ana kullen Coronovirus. Duk wani litta-fi an daura shi a kan wannan kwamfutan hannun.
Ai ni na ma fi son komfutan hannun, domin ba sai na shiga shafin yanar gizo ba, kuma zan iya cajin sa da hasken rana.

# Na'urar karanta littatafai

Na'urar karanta littatafai wata na'ura ce mai aiki da wutar lantarki da ta ke adana dinbin littatafai na kyauta wanda kowa da kowa zai iya amfani da su, har a wuraren marasa galihu. Ana kamanta ta da na'urar karatun e-book da ke tara dubunnan littatafai a lokaci guda, wanda girmansa bai wuce 'yar takarda ba. Idan batirinta ya cika, sai ta dauki makonni ta na aiki, kuma ta fi wayar salula ko komfutar hannu dadin amfani. Alal misali, Na'urar World Reader ta na bada dama a karanta  littafai masu kyau a ko ina a Duniya kuma a kyauta, ba tare da an bukaci intanet ba.

Misalin na'urar karanta littatafai shi ne Amazon Kindle Paper White wanda farashinsa bai wuce N15, 000 a kantunan yanar gizonmu na gida irinsu Jumia ko Konga.


Yaya Muda, don Allah za ka iya taimakawa ka daura mun jadawalin World Reader a na'urar karanta littatafai? Ina so in karanta labaran wasanni, littafan boko, na siyasa, da labaran age da sauransu.
Ba damuwa. Za ma ki iya karanta wasu littatafan a harsuna 44 na duniya, kuma har 70. Ba sai kin yi amfani da intanet ba.


Yanzu tunda na samu manhajar, zan iya kamo Zuri da Zara a littafin adabin ingilishin da su ke da shi a na'urar su mai kwakwalwa da kuma kwamfutar hannnu.

# Na'urar shiga Duniyar badini (VR)

Virtual reality hanya ce ta zuwa wata Duniyar badini ta hanyar amfani da karfin fasaha. Idan aka yi amfani da lasifikar kai watau 'Headset', za a iya hango wata Duniya ta dabam, kuma har ka ji tamkar ka na cikinta, ko kayi wasanni kamar ka na can da gaske. Virtual Reality fasaha ce ta zamani da ke ba yara damar koyon komai a wata Duniyar, amma su na zaune a inda suke. Wannan na'ura ta na suranta abubuwa na asali, ta maida su tamkar a zahiri a wata Duniyar dabam, wanda ke ba mutane damar su shiga can ayi da su.


Malam, muna neman taimakon ka domin yin gwaje-gwajen kimiyya, amma ba kayan aiki a makaranta.
Ai ba sai ka damu da wannan ba. Ba ka taba jin labarin VR ba?
Malam ka na nufin Virtual Reality?


Ga shi nan na ganni a cikin dakin yin gwajin kimiyya.
Ga ni ina rike da kwalaben gwaji a hannu na
Barkanku shigowa dakin gwajin ilmin sunadarai!




Yara na iya daukar ilmi daga talabijin ta hanyar kallon bidiyoyi masu dauke da bayanai ko shirye-shiryen bidiyo da malamai za su iya nunawa a lokacin darasi. Gwamnatoci za su iya tsara shirye-shiryen karatu da za a watsa a gidajen talabijin da ake da su. Malami ko mai karantarwa zai iya haska shiri a tashar talabijin mai kamar ajin karatu, sai masu neman ilmi su rika bibiyar shi kai-tsaye ko kuma a haska wani shirin karatu da aka dauka a baya. Ta hanyar darasin da ake yi, yara za su iya koyan komai a ko ina, har a kauyukan da suke da wahalar a iya shiga.


Malama ina da tambaya. Wai shin meyasa ki ke daukar bidiyon wannan ajin?
Yanzu da za a rufe makarantu, wannan bidiyon za a haska su ne a gidan talabijin domin ku da sauran dalibai da ba su zuwa makaranta. Za ku iya zuwa tashar kullum karfe sha-biyu domin ku kalla.
Ai ko mun gode sosai malama. Na ji dadi matuka tunda za mu iya ganin ki kuma har mu yi tamabay a karshen darasin.


TUNE IN TO WATCH EVERY
DAY BETWEEN 12PM AND
2PM. You can send your ques
tions after the lessons to
07099887766
Yanzu tun da na dauki bidiyon duka darusa na 36, zan iya turawa manajan gidan talabijin domin a yada su.


Ina matukar san wannan shirin. Malamar nan tana bayani sosai sai ka ce a cikin aji mu ke.
Ai ni yanzu na gane darasin Algebra, kuma zan iya yin Linear equations da kaina.
Ni dai ina da tambaya a kan Quadratic Equation.
Za ki iya tura tambayar ki zuwa ga 07099887766 bayan an gama darasin.

# Budaddun kafofin daukar karatu

Budaddun kafofin daukar karatu na OER su na nufin duk wasu kayan karatu da malamai da dalibai za su iya samu a cikin sauki, su yi amfani da su, su yada su, su cigaba da aiki da su. Ba tare da biyan sisin kobo ba, dalibai za su iya amfani da wadannan kafofi. Misalan kafofin da suke bada dama a samu kayan karatu a kyau sun hada da; Wikipedia, Wikimedia commons da Wikibooks.


Malam mai bautar kasa, ta ya za ka rika koyawa dalibai karatu bayan wannan kauyen ba su da intanet?
Direba ai ina da kayan koyarwa da zan iya amfani da su ba tare da yanar gizo a waya ta ba.


'Dan bautar kasa, ka ce mana akwai inda za mu iya karanta littafai, da labarai, har mu kuma kalli bidiyoyi a kowace irin waya.
Kwarai kuwa, akwai su. Yanzu bari in nuna maku yadda zamu shiga Wikimedia a waya ta.




Amfanin rediyo wajen karatu ya fi yawa ne wajen yada bayanai da nishadantarwa domin ya na taimakawa wajen kai sako ga dinbin mutane a cikin al'umma. Baya ga cewa ba ya bukatar yanar gizo, akwai araha da rashin bata lokaci. Koyarwa da koyon karatu ta rediyo ya na yiwuwa ne idan dalibai suka maida hankali a lokacin da ake watsa shirin; su ke bin malami, 'yan makarantarsu da abokan karantunsu. 'Dalibai za su iya kiran shirin gidan rediyo, su jefawa malami tambaya ko su bada amsa. Gwamnatocin jihohi za su iya tsara shirye-shirye ko a dauki darasin 'yan aji daya zuwa shida, a yada su a tashoshin gidan rediyo a garuruwa.

Misalan shirye-shiryen karantarwa da ake yi a gidajen rediyo a fadin Najeriya

| Tashar rediyo | Rana da lokaci | Darasin da ake yi |
|---|---|---|
| Radio Nigeria Enugu 92.9FM | Litinin – Juma'a 11am – 12pm | Ajin firamare |
| Ekiti 91.5 FM | Litinin – Juma'a 3.10pm – 4pm | Ajin firamare |
| Wazobia FM 95.1FM | Litinin – Juma'a 12pm – 1pm | Ajin sakandare |
| Eko 89.7FM | Litinin – Juma'a 10:30am – 1pm | Ajin firamare na 3,4,5, da 6 |
| Freedom FM 99.5FM Kano | Laraba – Juma'a 11:30am – 12:30am | Ajin sakandare |
| Naija 102.7FM | Litinin – Juma'a 11am – 12pm | Ajin sakandare |
| Wazobia FM 95.1FM | Litinin – Laraba 11am – 12pm | Ajin firamare |
| Radio Gotel 91.1FM Yola | Litinin – Laraba 11am – 12pm | Ajin sakandare |
| Radio Lagos 107.5FM | Litinin – Alhamis 9am – 11.55am | Ajin firamare |
| Peace FM 102.5FM Borno | Talata & Laraba 09:30am-10:30am | Ajin firamare |

A kiyaye:

- Mafi yawan wadannan shirye-shiye sun yi aiki ne a lokacin da aka rufe makarantu tsakanin Maris da Oktoba, 2020. Ana sa ran an cigaba da yin da-dama daga cikinsu a gidajen rediyo har yau.
- Tashar Wazobia FM ta na Abuja, Kaduna, Jos, Minna, Lafia da Suleja.


Ga shi ina ganin Bibian da Bolanle su na karatu a gida, ni ma kuma ga shi ina son in yi amfani da rediyon baba domin sauraron nawa darasin.


Barka da zuwa tashar Learning on air. Sunana Sisi Nene, kuma a darasin mu na kimiyya a yau, za mu yi bayanin tsabtace muhalli.
Ka da ku manta ku kira wannan lambar 07099887766 idan an gama darasin domin ku yi tambaya. Za mu ba ku amsa a nan take.
Lallai wannan kai kace mutum ya na cikin aji ne. fadawa baba nima ya sayo mani nawa rediyon domin in cigaba da karatu a gida.

# GODIYA TA MUSAMMAN

## Wanda ya dauki nauyin wannan aiki

---

## WADANDA SUKA TAIMAKA & WADANDA SUKA BADA GOYON BAYA

## SANARWA

Aid for Rural Education Access Initiative (AREAi) ya tsara, sannan ya buga wannan takarda a karkashin shirin Education Digital Equity Initiative da UK FCDO's Prosperity Fund Digital Access Program ta dauki nauyi.

Cikakkiyar hakkin mallaka © Aid for Rural Education Access Initiative (AREAi).